# ABUBUWA GUDA BIYAR DA YA KAMATA KA SAN SU

1. GA ABIN DA ALLAH YA FURTA!
"Kamar yadda yake a rubuce cewa, 'Babu wani mai adalci, babu ko daya … gama 'yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga daukakar Allah" (Romawa 3:10,23).

2. GA ABIN DA ALLAH YA ZARTA!
"Duk wanda bai tsaya ya aikata duk abin da ke rubuce a littafin shari'a ba, la'ananne ne" (Galatiyawa 3:10).

"Wanda kuwa bai ba da gaskiya ba, an riga an yi masa hukunci, don bai gaskata da sunan makadaicin Dan Allah ba" (Yahaya 3:18).

3. GA ABIN DA ALLAH YA TANADA!
"Almasihu ya fanso mu daga la'anan nan ta shari'a da ya zama abin la'ana saboda mu, domin a rubuce yake cewa, 'Duk wanda aka kafa a jikin itace, la'ananne ne" (Galatiyawa 3:13).

"Almasihu ya mutu domin zunubanmu, kamar yadda Littattafai suka fada." "Saboda kaunar da Allah ya yi wa duniya har ya ba da makadaicin Dansa, domin duk wanda ya gaskata da shi kada

ya halaka, sai dai ya sami rai madawwami" (1 Korantiyawa 15:3; Yahaya 3:16).

4. GA ZARAFINKA!

"Amma duk iyakar wandanda suka karbe shi, wato masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah" (Yahaya 1:12).

5. GA IYAKACIN BEGENKA!

"Wanda ya gaskata da Dan, yana da rai madawwami. Wanda ya ki bin Dan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi" (Yahaya 3:36).

"Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto" (Ayyukan Manzanni 4:12).



Free tracts and biblical counsel available by request. Write:
**Word Of Truth,** P.O. Box 1126, Kaduna, Nigeria.